Kaɗai an aikoni ne dan in cika manyan ɗabi'u

Daga Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: «Kaɗai an aikoni ne dan in cika manyan ɗabi'u».
[Hasan ne] [Bukhari a cikin Al-Adab Al-Mufrad da Ahmad da Baihaki suka ruwaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agate shi - ya bada labarin cewa kaɗai shi Allah - Mai girma da ɗaukaka - Ya aikoshi ne dan ya cika kyawawan ɗabi'u; inda aka aiko Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - dan cika abinda ya gabace shi na manzanni, kuma mai cika kyawawan ɗabi'un larabawa, sun kasance suna son alheri kuma suna ƙin sharri, masu mutunci ne da karamci da gabata; sai aka aiko Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - dan cike abubuwan da suka gaza da ke cikin ɗabi'unsu, kamar alfaharinsu da nasabobi, da girman kai, da wulaƙanta talaka da wanin hakan.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/66233